NIGERIAN ELECTRICITY REGULATORY COMMISSION

# KA'IDA NO: NERC-R-001-2023

## KAIDOJIN HUKUMAR KULA DA WUTAR LANTARKI TA NAJERIYA

**CIKIN AIKIN HUKUMAR KULA DA WUTAR LANTARKI TA NAJERIYA MAI TAKEN (HUKUMAR) A SASHI NA 80 DA 96 NA DOKAR DA AKAYIWA GARANBAWUL (DOKA) DA WASU BANGARORI, HUKUMAR TA SAMAR DA WADAN NAN KAIDOJIN.**

# TSARIN KOWANNE SASHI.

## SASHI NA DAYA

**Bai Daya**

1. Farawa
2. Manufa
3. Yadda za'a yi amfani da wadan nan kaidoji.
4. Sauyi da yin gyara.
5. Yadda za'a gyara abubuwan da suka shige duhu.
6. Inda za'a mika batutuwa
7. Ambato/Lissafi
8. Fassara.

## SASHI NA BIYU

**Hanyoyin bi wajan hadi ko yanke ayyukan wutar lantarki.**

9. Yadda za'a Hada/Gamuwa

10. Tsawirar hadawa/gamuwa

11. Kayayyakin aikin hadawa.

12. Hanyoyin hadawa ayyukan lantarki.

13. Lokaci hadawa.

14. Abubuwan da sabawa biyan kudi.

15. Taswirar hadawa.

16. Bukatar aiki ga wani adireshi dake kan tsarin.

17. Wajuban kamafanin rarraba wuta wajan jona sabuwar bukatar lantarki.

18. Sabon hadi.

19. Sabbin manufofin kamfani rarraba wuta wajan jona sabon bukatar lantarki.

20. Katse bukatar lantarki.

21. Sharuddan katse bukatar lantarki.

22. Kin yin biyayyar abokan hulda wajan bayar da bayanan kai ko tsaro na ajiya.

23. Yancin abokan hulda na bukatar Dakatarwa.

24. Sanarwar dakatar da samar da lantarki.

25. Abubuwan da suka haramta samar da lantarki.

26. Yadda za'a yi gyara wajan dakatar da samar da lantarki bisa kuskure.

27. Sake samar da hanyar samuwar lantarki.

## SASHI NA UKU

**Yadda mita ke aiki,Nawa take caja,Karban kudi da kula da kudin aikin lantarki.**

28. Yadda mita take aiki.

29. Karshen aikin mita.

30. Wata hanya ta musamman na aikin mita

31. Kudin da ake Caja.

32. Kudaden caja na karshe.

33. Katse ka sakamakon rashin biyan kudi.

34. Sauran kudaden biya na lokaci zuwa lokaci.

35. Samar da lantarki ba akan mita ba.

36. Daidaita kudaden biya.

37. Hanyar biyan kudi.

38. Kula da  Bashi.

39. Tsaron ajiya.

40. Sabunta zubin tsaro na ajiya.

41. Tsarin bi wajan biya a gaba.

42. Yadda za'a dawo da kudin da aka biya bisa kuskure.

**SASHI NA HUDU**

**Hanyoyin bi wajan kula da korafe korafen kwastoma da kula dasu.**

43. Samar da sashi na kula da koken kwastoma.

44. Dokokin bangaren.

45. Cire mamban bangaren.

46. hukunci bangaren.

47. Sanarwa a bangaren aiki na kamafanin rarraba wuta.

48. Hanyoyin bi wajan shigar da korafi.

49. Koken da bangaren ke saurara.

50. Hanyoyin bi wajan sauraron korafi a bangaren.

51. Hukunci bangaren

52. Daukaka kara.

53. kai rahotonni ga hukumar.

## SASHI NA BIYAR

### Tsarin aikin Kwastoma

54. Mayar da bada  lantarki ga kwastoma.

55. Yadda za'a dora sabon kwastoma.

56. Iya adadin da ake caja.

57. Sanarwar samun tangardar lantarki.

58. Korafi kan karfin lantarki.

59. Samun Hargitsin Mita.

60. Sake bukatar lantarki bayan an dakatar dakai sakamakon rashin biya.

61. Daidaita Mita.

62. Sauraron koke kan mitar da ba'a kai ga biya ba.

63. Tsarin da mita take aiki

64. Togiya.

65. Kula da tsarin kowanne aiki.

66. Bayyana tsarin kowanne aiki.

## FASALI/TSARIN AIKI

1. 1.Jadawalin hadi
2. Cikakkun bayanan kudi.
3. Taswirar koken kwastoma.
4. Takardar korafi ta 1
5. Takarda ta 2.
6. Takardar kula ta wata.

**SASHI NA DAYA**

**Bai Daya**

1. (1)Wadanan kaidoji dole ne suzo a daidai lokacin da hukumar ta amince da su.

   (2)Dole ne kaidojin su zamo dauke da sa hannun Shugaban hukumar,wanda hakan ne zai bata damar wanzuwa.

2. (1) Manufar wadan nan kaidoji shine samar da tsarin tafiyarwa wanda yazo daidai da dokaki kamar haka...

a. Hado kan dukkanin wasu kaidojin hukumar na kare hakkin kwastoma a bangaren masana'antar lantarki (NESI) zuwa abu daya.

b. Karfafa jadawalin kariya kwastoma a NESI.

c. Bunkasa samar da damar lantarki a NESI.

d. Jerawa da kuma sabunta tsarin kula da kwastoma a NESI wanda zaiyi daidai da tsarin da ake amfani dashi a duniya.

e. Kare hakkin tsarin rarrabawa na kwastoma ta hanyar fitar da adadin samar da kowanne aiki.

3. Wadan nan kaidoji ya shafi dukkanin masu lasisi da damar mallaka na rarraba lantarki ga kwastomomi,da kuma kwastomomi da masu rarrabawar zasu basu lantarki.

4. (1) Hukumar ta soke wadan nan kaidoji kamar haka...

(a) Tsarin kula da Koken kwastoman hukumar kula da lantarki ta najeriya

(b) Yanayin aikin Mitar hukumar,kudin da ake caja,karban kudi da kula da harkar kudin samar da lantarkin.

(c) Tsarin hadi da katse aikin samar da lantarkin hukumar.

(d) Yanayin hubbasan kwastoma ga kamfanonin rarraba lantarki.

(e) Tsarin hukumar lantarki ta najeriya wajan cazar kudi samar da lantarkin.

5. Hukumar zata iya gyara ko soke baki daya ko wani bangare na wannan kaidoji.

a. Duk inda aka samu wani cikas a bangaren kaidojin, hukumar zata iya bawa kamfanin rarraba lantarki ko ta dauki mataki,ba tare da dagewa akan dokar ba wanda zai janyo kari koma janye matsalar da ake batu akai.

6. Hukumar zata iya bada umarni ko daukar mataki ya danganta da abunda doka ta tanada akan kaddamar da wanna tsari.

7. Za'a iya daukar wannan kaida a matsayin kaidar kariyar kwastoma ta shekarar 2023.
8. (1) in ba har an fito an bayyana kai tsaye a wadan nan kaidoji ba...

(a) Kalaman dake tafiya da kowanne irin jinsi,wanda ya hada da sauran jinsin,dana mutum daya da mai jumulla.

(b) Kalmomi ko yanayi da akayi amfani dasu a wadan nan kaidoji,amma ba'a bayyana su ba,suna amfani ne da ma'ana daya koda ba'a saka su cikin doka ba.

(c) duk wani batu akan wanna tsari wanda ya hada harda wanda akawa gyara/Garanbawul,ko sake kirkirar shi,ko ma sauya shi daga lokaci zuwa lokaci.

(d) Idan har lokacin da aka ware a wannan kaidoji ya zamo rana bata aiki ba,to za'a iya dakatawa har sai ranar aiki ta gaba.

(2) A wannan tsari in ba har an samu sauyi ba...

"Doka" Wacce ke nufin dokar lantarki da akayiwa gyara.

"Shaidar gabatar dakai da aka amince da ita" Hakan na nufin duk wata shaidar amincewa ta Gwamnati ko kamfanin rarraba lantarki.

"Hukumar data Dace" Hakan na nufin duk wani mutum ko jami'i da kamfanin rarraba lantarki ya bawa damar hada lantarki.

"Wuraren rarraba lantarki"Hakan na nufin wurin da kamfanin rarraba lantarki ya amince dashi wajan bada lasisin raba lantarki.

"Takardar kudi" Hakan na nufin wani rubutu dake dauke da bayanin bashin da kamfanin rarraba lantarki ke bin kwastoma kuma dole ya zama akwai bayani na kaidoji a ciki.

"Hukuma' Hakan na nufin Hukumar Kula da Wutar lantarki ta Najeriya.

"Kwastoma kasuwanci" Hakan na nufin kwastoman dake amfani da lantarki domin buƙatun yau da kullum,hakan ya hada amma bai takaita kan Kasuwanci,Makarantu, Masana'antu, Gwamnati ko Wata cibiya ba.

"Mai Shigar da Korafi" Hakan na nufin mutum ko wani jami'i dake da alhakin rubuta korafin da aka shigar akan kamfanin rarraba lantarki.

"Korafi" Hakan na nufin bayanin koke da kwastoma akan samar da lantarki na kamfani.

"Jam'in Kula da Korafi" Hakan na nufin mutumin dake da alhakin kula da bangaren shigar da korafe korafen kwastomomi na kamfanin rarraba lantarki.

"Bangaren kula da rancen kudi" Hakan nufin hanyar bawa kwastoma rance,da yadda zai biya daidai akan lokaci da kuma tabbatar da kwastoman yabi kaidojin bashi na DisCos.

"Kaidojin kula da basussuka" Hakan na nufin wasu kaidoji na DisCos dake bata damar kula da basussukan ta

"Kwastoma" Hakan na nufin mutumin da yayi rijista da kamfanin rarraba lantarki domin samar da wutar ga muhallin sa.

"Bangaren kula da korafe korafen kwastomomi" Hakan na nufin wani sashi da aka ware domin sauraro da kuma magance koken kwastomomi.

"Samun Sabani da Kwastoma" Sabanin da ake samu inda kamfanin rarraba lantarki ke kin amincewa ko karban wani koke na kwastoma.

"Aibi" Hakan na nufin duk wani akasi,kuskure da aka samu a adadi ko inganci na aiki,wanda ke karkashin kula ta kaidoji kuma yazo a koken kwastoma.

"Kasawa" Duk wani kuskure,gazawa,karanci ko akasi a bangaren ingancin aiki,ko yanayi da aka bukaci gabatar da aiki a karkashin wata doka ko kaidoji da kamfani ta gaza cikawa a bangaren bada lantarki ga kwastoma.

"Kamfanin rarraba lantarki" Kamfanin da hukumar ta amince hada da bawa lasisin bada lantarki ga abokan hulda.

" Samar da Lantarki" Hakan nufin bada lantarki da duk abunda ya shafe shi ga kwastomomi.

"Dandalin Tattaunawa"Hakan na nufin wata tawaga da aka kafa domin sauraron koke da kuma magance su tsakanin kamfanin rarraba lantarki da kwastomomin su.

"Gwamnati" Gwamnatin tarayya ko ta jaha ko wata hukumar dake karkashin tarayyar ko jaha.

"Matsakaicin kwastoma" Sune kwastomomi dake son kansu wajan amfani da muhallansu da wata manufa maimaikon abunda aka sani na yau da kullum.

"Mamba" Na nufin mamban tawaga ,ko kungiyar hakan ya hada mai ci.

" Aikin Mita"Hakan na nufin hanyar da ake kula ko bincike mitar wuta domin ganin abunda take caja kan kowanne kwastoma dae saurane su.

"Karamar Matsala" Hakan na wannan nufin duk wata yar karamar matsala ta wuta da za'a iya magance tsakanin Awanni biyu da sanin kamfanin rarraba lantarki.

"Wata" Hakan na nufin kwanaki 30 na cikin kalanda.

"NEMSA" Hakan na nufin Hukumar Kula da ayyukan lantarki  ta najeriya wacce aka kaddamar cikin doka a shekarar 2015.

"NESI" Na nufin maaikatar bada lantarki ta najeriya.

" Mamba Mai Ci' Na nufin mamban dake tawaga dake jagorantar tarurruka da wasu Tattaunawa.

**SASHI NA BIYU**

**Hanyoyin bi wajan hadawa da katse samar da wutar lantarki**

9. 1 Dole ne mahadar wutar kwastoma ta zamo kodai ta sama ko ta kasa.

2 Tsarin na bukatar ya zamo anyi shine daga muhallin Kwastoma zuwa na alumma hada da saka mita hakan ne ya samar da..

a. Duk wata wuta dake zuwa bisa karancin karfi data hadar da yankakiyar wayar alminiyom PVC,MCB,cire fuse da saka pin da kuma...

b. Mita da abunda ya dangance ta anyi bayani na musamman a bangaren lambobin su.

10. 1 Damarmakin samar da lantarki da kamfani ya kamata ya bawa kwastoma.

a. Hanyar wuta ta sama mai fuska daya

b. Hanyar wuta ta sama mai fuska uku.

c. Hanyar wuta ta kasa mai fuska daya.

d. Hanyar wuta ta kasa mai fuska uku.

e. Aiki na musamman (A inda aka samu akasi wurin da kwastoma yake yayi nisa da guri mafi kusa na samar da lantarki.

f. Sanarwa ta 11KV link up high-tension

g. Samarwa ta 33KV link up high-tension.

2. Dole a samu amincewa daga hukumar a inda aka samu bukatar samar da lantarki sabanin wadan nan da aka lissafo.

3. Kamfanin rarraba lantarki zata bukaci amincewar ne ta hanyar mika bukatar hakan da cikakken bayani na irin kayan datake bukata kamat yadda yazo a mukalar data gabata.

11. 1 Kayan aikin da ake bukata domin hada lantarki (banda mita da danginta) daga wajan da lantarki take mafi kusa dole ne su zamo sun tafi daidai da tsarin farko na wannan kaidoji.

2. Girma da ingancin kayan aikin da ake bukata na hada lantarkin,ya danganta ne da yanayin tsari da kuma nisan da muhallin Kwastoma yake da inda ake bayar da lantarkin.

12. (1) Dole ne dukkanin wani tsarin hada lantarki ya zamo yabi kaidojin da aka fitar.

(2) Kwastomomin da suka bukaci a hada musu lantarki a muhallansu sune keda alhakin samar da kayan aikin da ake bukata,kamar yadda yazo daga tsarin da kamfanin rarraba lantarki ta amince dashi,Yayin da ita kuma kamfanin alhakin tane hada wutar tun daga Tushe har zuwa inda kwastoma yake.

(3) Dole ne jam'in bincike yaje ya duba muhallin Kwastoma daga inda za'a janyo masa wutar har zuwa kan mitar sa domin tabbatar da adadi da kuma ingancin kayan da ake bukata.

13. (1) Dole ne cikin Awanni 48 da samar da kayayyakin hada lantarki daga kwastoma, kamfani ta tabbatar da ta hada wutar lantarkin ga muhallin Kwastoma.

(2) Dole be kuma a tabbatar da an samar da Mita da danginta ga kwastoma domin ta fara aikin cajar shi adadin lantarkin daya sha.

14. (1) Ba'a Yadda kamfanin rarraba lantarki ta karbi wani kudi na zuwa duba muhalli ko gwajin lantarki a muhallin kwastoma ba.

15. Ana bukatar Dukkanin kamfanonin rarraba lantarki dasu mika takardar hada lantarki ga hukumar domin amincewa,hakan kuma dole ya kunshi bayanin wani irin hada lantarki za'a wa kwastoma kammar yadda aka lissafo su a baya.

16. (1) Kwastoman da yake bukatar a hada mishi wuta a muhallin dake akwai wutar zai...

a. Aika bukatar hakan bisa tsarin da kamfanin rarraba lantarki ta fitar.

b. Zai bi doka da sharuddan kamfanin.

c. Samar da duk abunda ake bukata na hada lantarki

d. Bayar da duk wata shaida da kamfanin ya bukata

17. (1) Kamfanin rarraba lantarki zai....

a. Bawa kwastoma duk wasu dokoki da sharudai a rubuce da zasu kai ga samar masa da lantarki.

b. Samarwa da kwastoma lantarki cikin Awanni 48 daya shigar da bukatar hakan kamar yadda yazo daga tsarin.

c. Tabbatar da duk wasu takardun kudin lantarki na dauke ne da sunan kwastoma.

18. (1) Kwastoman dake bukatar a hada masa lantarki a inda babu kamfanin rarraba lantarki kusa dashi zai.....

a. Shigar da bukatar hakan mai dauke da sunan sa,kuma bisa kaidar kamfanin rarraba lantarki.

b. Samar da dukkanin wasu abubuwan bukata daga gare shi.

c. Bayar da duk wata shaida da bayanan da zasu kai ga an riski adireshin sa.

d. Tabbatar da komai ya kammala kamar yadda yake zuwa bisa kaidar kowanne kamfanin rarraba lantarki.

19. (1) Kamfanin rarraba lantarkin da zata saka lokaci domin saka mita ga kwastoma a tsakanin lokacin da aka bayyana a wannan bigire kadai ne idan ..

a. tsarin samar da lantarkin a Kwastoma yazo daidai da tsarin da hukumar ta amince dashi

b. Amincewar kwastoma game da rubutaccen kaidoji da tsare tsaren dake nuna kewaye da samar da lantarkin.

c. Amincewar saka sunan kwastoma akan takardar kudin wuta.

d. Kwastoma sai ya amince hada da biyan kudin hada lantarki.

20. (1) Kamfanin rarraba lantarki zata iya datse wutar kwastoma idan har yaki biyan basussukan dake kanshi na wuta ko kuma ya karya wasu kaidoji da dokokin kamfani.

(2) Dole ne abi wadan nan kaidoji kafin kamfani takai ga datse wutar lantarki kwastoma sakamakon rashin biya a lokacin da aka yanke masa....

a. Dole ne a bayyana ranar biya a cikin takardar.

b. Akalla ranar biyan zai zamo kwanaki goma daga ranar da aka kawowa kwastoma takardar kudin wuta. Za'a kawo mishi takardar ne har gida ko kuma a tura mishi ta sakon karta kwana ko email bisa amincewar kwastoman.

c. Tazarar kwanakin dake tsakanin wa'adin ranar biya da yanke wutar kwastoma idan ya gaza biya kwanakin aiki biyu ne rak.

d. Dole ne kamfanin rarraba lantarki ta tabbatar a cikin jadawalin ta cewa kwastoma bai biya kudin wuta ba.

3. Duk wata takardar datake dauke da bukatar gyaran kuskure akan batun biyan kudin wuta dole ne ta zamto tana da kwanan wata biya,kwana 10 daga lokacin da aka bawa kwastoma ainihin takardar kudin wuta.

21. 1 Batare da son zuciya ba kamar yadda yazo a sashi na 20, Kamfanin rarraba lantarki zai iya datse wutar kwastoma bisa wadannan dalilai...

a. Satar wuta daga kwastoma.

b. Idan aka ga cewa tsarin jan wutar kwastoma yana da hatsari ga ingancin samar da lantarki ga sauran kwastomomi da kayayyakin ta.

c. Idan kwastoma yaki amincewa jam'in kamfani ya duba yanayin aikin mitar dake muhallin sa.

22. Kamfanin rarraba lantarki zai iya kin hadawa kwastoma wuta idan har yaki bayar da bayanan da ake bukata ko kin biyan kudin tsaro.

23. (1) A duk lokacin da kwastoma ya bukaci kamfani ta datse wutar shi, za'a iya yin hakan kadai bayan an tabbatar da yin hakan bazai shafi sauran mutanen da suke muhalli daya ba,wanda kuma suke bukatar cigaba da amfani da wutar.

(2) Dole kamfani ta tabbatar da ta saka ido akan adadin wutar da kwastoman daya bukaci a datse nashi wanda babu damar yin hakan yake sha.

(3) Daga lokacin da aka samu yankewar lantarki Kamfanin bata da hurumin cajar kwastoma wutar kwanakin da hakan ya faru kamar yadda yazo karkashin sashi na 23(1).

24. (1) a duk lokacin da kamfani ta katse wutar kwastoma to zata bar masa takardar shaidar hakan bisa shawari kamar haka....

(a) Lokaci da kwanan watar katse wutar

(b) Dalilin katse wutar.

(c) Abunda kwastoma zaiyi domin a dawo masa da wutar.

(d) Lambar waya,da adireshin tawagar kamafanin da sune suke da alhakin mayar masa da wutar.

25. (1) Kamfani bazata yankewa kwastoma wuta sakamakon rashin biya ba idan har....

(a) kwastoma ya biya abin da ake binshi.

(b) kwastoma ya shiga wani tsari na biyan wuta da kamfani kuma yana kan bin tsarin.

(c) Kwastoma ya shigar da korafin mika mishi takardar rashin biya (Bayan kuma ya biya) sanna a ba'a kai ga magance matsalar ba.

2. Kamfani bazata yanke wutar muhallin data san cewa ana cigaba amfani da na'urar dake taimakawa rayuwa ga mara lafiya ba.kwastoma zai iya shiga wani tsari na wannan biyan kudin wuta da kamfani,sanna ita kuma kamfanin zata iya bin wata hanya halstaciya wajan warware bashin datake bi.

26. (1) Duk kwastoman da aka yankewa wuta bisa fatali da wadan nan dokoki,dole ne a biyashi diyya.

(2) za'a bawa kwastoma bashin wuta iya adadin yadda suke sha na tsawon watannin uku ko har na tsawon kwanakin da aka saba mishi.

27. (1) Kamfani zata mayarwa da kwastoma wuta karkashin wadan nan kaidoji idan har....

(a) Aka samu kwastoma yana cikin wani tsari na biyan kudi wanda hukuma da kuma kamfani ya yarda dashi.

(b) Rashin samun tabbas na cewa kwastoma na cikin wani tsari tare da kamfani na biyan kudi.

(c) Aka samu salon jan wutar kwastoma yana da hadari ga kamfani ko makotan sa da suke tar sai kum....

(i) Ya gyara matsalar da aka yanke wutar domin ta.

(ii) Wata cibiya da aka amince da ita tazo ta duba da kuma tabbatar da ingancin layin wutar shi

(iii) Ya biya kudin da kamfani ta caje shi,ko kuma aka samu yarjejeniyar shiga tsarin biyan kudin.

d. aka samu kwastoma dakin amincewa a duba mitar dake muhallin sa,Amma daga baya ya amince da kuma biyan kudin sake mayar masa da lantarkin.

## SASHI NA UKU

## Kudin da mita ke Caja,Karban kudin wuta a hannu,da kula da basussukan wuta

28. (1) Kowanne kamfanin rarraba lantarki dole ne ya zama yana duba akan yadda mitar dake yankin dayake aiki take kowanne wata ko kuma sau daya cikin wata uku.

(2) Duk lokacin da akayi rashin Sa'a jami'i baya iya duba aikin mitar kwastoma dake muhallin sa,to yabar rubutaccen sako akan hakan ga kwastoma.

(3) Idan aka samu wani yanayi da kamfani ya kiyasta adadin wutar da kwastoma yasa,ya tabbatar da hakan yayi daidai da abunda kwastoman je tunanin yayi amfani dashi ba tare da an samu akasi ba.

(4) Tsarin da kamfani ke amfani dashi wajan kiyasta wutar da kwastoma yasha a wasu lokuta na musamman ya kasance ya samu amincewa daga hukumar.

29. (1) Kwastoma zai iya bukatar kamfani daya mishi duba na karshe akan kudin dake kan mitar shi idan har bukatar sauya muhalli ta kamshi,da kuma adadin da ake ganin zai iya sha a gaba.

(2) Da zarar kwastoma ya mika wannan bukata ta duba masa mitar sa, kamfani zata saka lokaci domin zuwa ta gabatar da hakan.

(3) Idan aka samu akasi kamfani yaje amma bai iya duba mitar ba sakamakon wani dalili daga kwastoma, kamfani zata katse wuta tare da bada takardar kudin wuta ta karshe ga kwastoma kuma shine zai biya duk bashin da ake binshi wanda hakkin kamfani ne ta karba, ba'a yadda kamfani ta dorawa sabon Dan haya dazai kama muhallin bashin wannan mita ba.

(4) Idan kuma aka samu akasi kamfani ce ta kasa cika Alkawarin lokacin data daukarwa kwastoma na duba mitar sa, alhakin wutar dake kan kwastoma ta zuwa lokacin daya saka ne na canza muhalli a takardar daya mikawa kamfanin

(5) Sabbin yan haya kuma zasu tuntubi kamfanin rarraba lantarki a ranar da suka tare,ita kuma kamfani zata mayar musu da wuta,sannan kudin su zai fara aiki ne daga ranar da wutar ta samu gare su.

(6) Kwastoman da kamfani zata amince dashi shine mamallakin muhallin ko wanda aka wakilta don kula da muhallin wanda shine zai dinga biyan duk wasu harkokin kudin wuta ga kamfani.

(7) Akwai bukatar samar da kyakkyawan banbanci tsakanin mamallakin muhalli da kwastoman kamfani saboda batun karban takardun da biyan kudin wuta.

30. (1) Kamfani ko kwastoma na iya shigar da bukatar sake duba aikin mita daya gabata idan akwai kuskure ko kuma tana aiki ba daidai ba.

(2) Kamfani bazai kai takardar biyan kudi sau biyu ga kwastoma daya a lokaci daya ba.

(3) Duk wasu batutuwan dake jikin takardar biyan kudin wutar su zamo an rubuta su ta yadda kwastoma zai gane kuma su zama suna dauke da kaidoji na tsari na biyun wanna kaidoji.

32. (1) Kamfani zai bayar da takardar bashin da ake bin kwastoman dake kokarin barin wurin da kamfanin yake domin biya kafin tashi.

(2) Ba'a yarda kamfani ya kara cajar kwastoma ba,bayan kuma an hour rigada an basa takardar karshe ta wutar.

33. (1) kamfani zai yi amfani ne da adadin da mita tasha a lokacin da aka datsewa kwastoma wuta,kuma takardar zata nuna adadin abunda yasha da wanda ake binsa har zuwa lokacin da aka datse masa wutar.

(2) A duk lokacin da aka katsewa kwastoma wuta kuma aka bashi takardar wutar dake nuna adadin dayasha har zuwa lokacin da aka katse wutar, kamfani bazata sake cajar wannan adireshin ba har sai in an sake mayar da wutar.

34. (1) A bigire na musamman ne kadai kamfani zai iya cajar kwastoma wani karin cajin a yayin biyan kudi.

(2) An fadi wannan bigiren a karamin sashi na (1) wanda zai ya hada da bukatar yin gyara akan takardar farko da aka gabatar ko kuma idan kwastoma ya bukaci hakan.

35.A inda ya kasance kuma babu mita bare a duba adadin wutar da kwastoma yasha, kamfani zata iya kiyasta adadin bisa tsarin da hukumar ta shinfida.

36. (1) Kamfani dole ne ta duba mitar kwastoma idan ya bukaci hakan.

(2) Yayin da ake kan dubawa kamar yadda aka fada a karamin sashi na (1), kwastoma zai biya iya adadin da kwastoma irin sa dake yankin yake biya, har na tsawon watannin sha biyu da suka gabata,idan kuma ya kasance baya yankin na tsawon watannin sha biyu to za'a caje shine da irin adadin da yake sha idan ya kasance dama shi kwastoman Kamfani ne tun baya.

(3) idan aka gano bill wanda ya wuce na lokaci daya,to kwastoma zai biya kudin kamar yadda yazo a karamin  sashi na (2)

(4) Idan kuma aka gano cewa binciken da ake akan takardar biyan kudi daidai ne, kwastoma zai iya amincewa da hakan ya kuma biya kudin da ake binsa,ko kuma ya bukaci a sake duba masa mitar ta hanyar amfani da lambobin ta.

(5) Idan kuma gwajin Mita da NEMSA ko Wata cibiya da aka yadda da ita ya nuna komai yazo daidai da abunda lambobin mitar ya nuna, Kwastoma zai biya kudin bashin dake kan mitar.

(6) Idan kuma binciken ya nuna cewa tabbas akwai kuskure to kamfani zata yi gyara akan bill din.

(7) idan kuma aka samu inda kamfani ta caji kwastoma fiye da kima to zata mayar masa da kudin sa a bigire na gaba da zasu hadu.

(8) Idan kuma aka samu inda kamfani ta caji kwastoma kasa da abunda ta saba zata sanar da kwastoma akasin da aka samu a rubuve daga nan kuma sai ta sake gyaran.

(9) Adadin da kamfani zata karba kamar yadda yazo a karamin sashi na (8) sun hada da..

(a) Idan har caji kasa da abunda ta sabawa kwastoma yazamo laifin daga gare tane,to zata caje shi iya adadin abunda ta dinga rage masa domin mayar da adadin cikin amma kar ya wuce watannin uku.

(b) A inda kuma  aka samu wani dalili,to kamfani zata tabbatar da amsar duka wadan nan bashi ne a tsakanin watanni shidda farawa daga lokacin data sanar da kwastoma lamarin.

10. (1) Kamfanin rarraba wutar lantarki zata.....

(a) Kar kamfani ta canja adadin da aka samu ta kowacce fuska,ko cajin kwastoma wani adadi.

(b) bawa kwastoma lokaci na biyan kudin da ake binshi,amma kar ya wuce adadin lokacin da aka gano matsalar.

37. (1) Kamfani zata iya karban biyan kudin wuta ta wadan nan hanyoyi....

(a) Karbab madarar kudi daga kwastoma a duk wata cibiya ta biyan kudin,sai dai idan har inda hukuma ta dakatar.

(b) Shaidar biya daga banki.

(c) Shaidar biya daga bankunan da hukumar ta amince ayi biya daga cikin su.

(d) Tsarin biya na bashi da hukumar ta amince dashi a cikin kaidojin ta.

2. kamfani zata iya karban duk wani biyan kudin wuta daa akayi gabannin lokacin biyan,ta hanyar karban shaidar hakan da adana shi.

3. idan kwastoma ya biya kudi,to kamfani zata bashi cikakkiyar Shaidar hakan mai dauke da...

(a) Cikakken sunan kwastoma.

(b) Adireshin sa.

(c) Lambar Asusun dayayi biyan

(d) Adadin daya biya.

(e) da kuma sauran bayanan da kamfani taga bukatar bayyana su.

38. (1) kowanne kamfanin rarraba lantarki dole ne ya fitar da tsari na bada bashi gabanin tunkarar hakan.

(2) Dole ne a mika dukkanin tsarin ga hukuma domin amince dashi gabanin fara aiwatar da hakan.

39. (1) Kamfani zata iya bukatar kwastoman da ake binshi bashi akan mitar shi daya biya wani adadi a matsayin tsaro gabannin kudaden gaba,hakan kuma za'a iya aiwatar dashi ne kadai akan kwastoman da yake da tarihin bashi akan mitar sa.

(2) Kudin da kamfani zata bukata daga kwastoman kar ya wuce na adadin wutar dayake na tsawon watanni biyu.

(3) Kamfani zata sake duba akan kudin tsaron da aka biya,idan adadin bai kai abunda kwastoma kesha cikin watanni biyu ba, kamfani zata iya sake bukatar kwastoma ya sake biya amma kar ya wuce adadin data yi magana a baya.

(4) Idan kuma aka samu kudin ya wuce abunda kwastoman yake sha cikin watanni biyu,to kamfani cikkn kwanakin aiki 10 zata yi rubuta ga kwastoma ta mishi bayani da kuma mayar mishi da kudin daya hau kai.

40. (1) batare da cin karo da karamin sashi na (4) cikin saahi na 39 ba, kamfani zata iya rike kudin tsaro na kwastoma har sai yabar muhallin sa,daga baya saintayi sabin lissafi ta fitar da lissafin asusu na karshe.

(2) A inda kuma I aka samu kuskure wajan sauran kudin kwastoma daya rage, kamfani zata iya rubuta ga kwastoma ta mishi bayani hada da mayar mishi da sauran kudin shi kwanaki 10 kafin ranar da aka kai mishi bill

(3) Idan kuma inda aka samu matsalar dama akwai bashi akansa, kwastoma zai biya dukkan adadin bashin wuta dake kansa, kwanakin aiki 10 bayan kai mishi bill.

41. (1) Duk inda kwastoma ke samun matsala wajan biyan kudin wuta a lokacin da aka saka,to zai tuntubi kamfanin akan Matsalar ,ita kuma zata samar mishi hanya ta biyan ko wani tsari,sai dai idan har kuma an taba samun shi da laifin kin bin doka yadda ya kamata.

(2) Tsarin biyan zai zama kodai kwastoma zai biya bashi ne da kuma kudin gaba dake kanshi,ko zai biya kudin dake kanshi na yanzu da kuma wanda zai zo gaba.

(3) A yayin lissafin kudin da kwastoma zai biya wanda ya hada dana gaba masu zuwa, kamfani ba zata iya canza adadin fiye da abunda kwastoma ke tsammanin biya ba.

(4) Yarjejeniya biya tsakanin kwastoma da kamfani tazamo a rubuce ga kwastoma na adadi da lokacin biyan.

42. Inda kuma aka samu kamfani ta gaza bin kaidar hukumar ta karban kudi a wajan and kwastoman da bashi da mita, kamfani zata mayar mishi da kudin daya hau akai a gaba.

**SASHI NA HUDU**

**Hanyoyin sauraron koke kwastomomi da kuma yadda ake tafiyar dasu.**

43. (1) Kamfanin rarraba wutar lantarki zata samar da bangaren sauraron koken kwastoma (CCU) a dukkanin bangarorin aikin ta domin saukakawa wajan mika koke a dukkanin kamfanin,CCU zata Zamo itace keda alhakin kula da korafe korafe.

(2) Dukkanin bangarorin sauraron koken dole ne su zamo bisa jagorancin Shuwagabannin maaikata da Ma'aikatan su kamar yadda yazo bisa tsarin kamfani,abun bukatar shine kawai a tabbatar da an saurari koken da kuma kawo gyara domin kyautata aiki.

(3) Dole ne kamfanin rarraba lantarki ya zamo ya kula da dukkanin korafen da aka shigar bisa tsarin shi a rubuce,daga nan sai su mika su ga hukuma domin amincewa.

(4) Dole ne kwastoma ko wakilin sa ya fara mika korafi ga CCU na kamfanin wuta,ita kuma kamfani ta tabbatar ta saka ido wajan bin diddigin magance ta.

(5) Kwastoma zai iya shigar da korafi ta hanyar kiran waya,ko tura sako, email ko wata hanya da kamfani ta samar domin ganin shigar da korafi wanda ya hada da call center da kafafen sada zumunta, kamfani zata samar hada da bada lambar waya,adireshin yanar gizo a yankin da take domjn samun saukin amsar korafe korafe

(6) Idan Korafin akan wani abu ne da baza'a iya rubuta shi ba, jam'in da akawa korafin zai nadi muryar ya kuma rubuta cewa shine ya ajiye korafi amma ta amfani da murya,daga nan kuma sai ya biyawa mai korafi korafin sa domin ya tabbatar da ba'a samu akasi ba.

(7) Dole ne a magance duk wasu korafe korafe bisa wadan nan kaidoji,Magance korafin tsakanin kwanaki sha biyar sai dai idan har batun ya hada daduba mita kona kudin biya wanda hakan kuma kar ya wuce wata guda.

(8) Idan aka samu akasin rashin magance matsalar a tsakanin kwanaki sha biyar, Kamfani zata aika a rubuce ga kwastoma dalilin rashin gyara matsalar sannan ta sake bukatar wasu kwanaki sha biyar din, sai dai idan bukatar dama mai daukar lokaci ce.

(9) Kwastoman da bai gamsu da yadda aka tafiyar da korafin sa ba daga bangaren sauraron koken kamfani,to zai iya mika koken zuwa ofishin tawagar hakan ta hukumar cikin kwanaki 30.

(10) A duk lokacin da aka samu sabanin fahimta tsakanin kwastoma da kamfani akan wani korafi to zasu iya tattarawa suje gaban tawagar hukumar.

44. (1) Hukumar zata bude ofishi domin sauraron koken kwastomomi daga kamfanin rarraba wutar lantarki.

(2) ofishin zai zamo a kusa da kamfanin rarraba lantarki,sanna za'a samar da Sakatare da sauran su domin tafiyar da aiki daidai.

(3) Ofishin tawagar zai zama yana da mambobin wucin gadi biyar,amma banda maaikata ko Yan uwan maaikatan kamfanin rarraba wutar lantarki a cikin tawagar.

(4) Za'a hada mambobin tawagar ne kamar haka.

(a) Masanin Sharia wanda keda sani a bangaren warware damuwowi kuma hukumar lauyoyi kasa tasan dashi.

(b) Masani a bangaren kudi mai shaida daga wata Ma'aikata ko kungiya da aka amince da ita a najeriya.

(c) Masani a bangaren wuta(injiniy) wanda keda shaidar kwarewa daga kungiyar injiniyoyi ta najeriya,ko mai kula da harkokin injiniyoyin.

(d) Maaikaci a bangaren kula da hakkin kwastoma (FCCPC).

(e) Maaikaci daga bangare mai zaman kansa wanda hukumar ta aminta dashi

5. idan aka yi rashin Sa'a wadan nan maaikatu basu turo wakilai ba,to hukumar zata iya samo wasu daga wasu maaikatun da aka amince dasu.

6. Mambobin tawagar zasu zabi shugaba da zai dinga kula dakomai,kuma ba bukatar sake zaben wani a karo na biyu.

45. (1) Za'a iya dakatar da Mamban tawagar daga zuwa ofishi idan daya daga cikin wadan nan ta faru.

(a) yayin fuskantar durkushewa

(b) Yayin tuhuma akan ofishi

(c) Zargin son kai akan abunda ya shafi aiki.

(d) Rashin iya gudanar da aiki a zahiri ko badini.

(e) Cin zarafi

(f) Gaza Halarta manyan tarukan tawagar guda uku.

2. Hukumar zata iya tsige kowanne Mamba na tawagar idan

(a) idan aka samu mamba ta banzatar da aikin sa wajan mai da hankali a abunda bai shafe shi ba

(b) Idan mambobin tawagar suka yanke wani hukunci daya ci karo da kaidar hukumar.

(c) Idan cigaba da aka zaman nashi bashi da amfani ga tawagar.

46. (1) Tawagar zata samar da wata kafa da zata dinga hada taron sauraron koke a yankin da kamfanin rarraba wutar yake.

(2) Hukumar zata saka ido kan adadin koken datake samu da kuma tabbatar da an magance su tsakanin watanni biyu da gabatar dasu.

47. (1) Hukumar zata fara gangamin wayar dakai kan aikin bangaren shigar da korafin kamfanin CCU da kuma wanda ke karkashin tawagar hukumar.

(2) Kamfani zai tabbatar da ya raba takardar tsarin yadda kowanne kwastoma zai iya shigar da korafi batare da ko sisin sa ba.

(3) Haka kuma za'a bayar da lambobin wayar da kwastoma zai iya samu kai tsaye na bangaren shigar da korafi ko tawagar.

(4) Duk wata takardar biyan kudi da za'a bawa kwastoma dole ne ta zamo tana dauke da adireshi,lambar waya, box office, adireshin email da kuma wannan jawabi.

"Duk kwastoman da ya shigar da koke ga kamfani rarraba wutar kuma ba'a karbi koken nasa ba,zai iya zuwa wannan ofishi dake karkashin hukumar kula da lantarki ta najeriya domin sake shigar da korafin."

(5) Samar da wannan dokoki da kaidoji ta kafar da za'a iya sauke su bada wahala ba,da kuma fassara su zuwa yare daban daban domin samun isar da sakon.

48. (1) Dole ne a mika duk wasu korafe korafe a rubuce da danganta su ga Shugaban tawagar,kamar yadda yazo tsari na 4 na kaidoji.

(2) A tabbatar da an kuma tura korafi ta email ko kuma a rubuce ga bangaren da ake bukatar kai Koken.

49. (1) Da zarar an samu korafi sakatare zai rubuta tare da shigar da bayanin komai harda lokacin da aka aiko da korafin.

(2) Sakataren kuma zai tura sakon ganin Korafin cikin kwanaki uku na aiki da samun sakon

(3) idan kuma Wata kungiya ko tawaga ta shigar da korafi a madadin kwastoma,dole ne korafin ya zamo yana tafiya da sahalewar kwastoman.

(4) Tawagar zata zauna tayi tunani ko zata saurari koken ko kuma yin watsi dashi cikin kwanaki 10 da shigar da korafi.

(5) idan ta amince da sauraron korafin zata duba wani iri ne cikin korafe korafen da yazo a kaidojin ta.

(6) Tawagar zata iya kin sauraron koken idan har ta gano rashin,inganci,hujjoji da karya a ciki.

(7) Idan aka ki amsa korafi to kwastoma nada yancin a rubuta masa tare da bayanin dalilin hakan cikin kwanaki biyar na aiki,da kuma sake bashi damar bayanin gamsasshe,haka kuma yana da damar daukaka wannan korafi zuwa ga hukumar idan ...

50. (1) Tawagar zata....

(a) Mika kofin takardar korafin ga jam'in CCU da kuma bashi umarnin kula sa batun cikin kwanaki aiki 10 ko kuma biyar ya danganta da irin korafi.

(b) Idan har bayan samun takardar korafi da jami'i yayi kamar yadda akayi bayani a sama,kuma bai yi wani abu akai ba,to hukumar zata iya wucewa gaba wajan sauraron koken kwastoma bisa...

(a) hujja mai karfi  da mai korafi ya gabatar mata

(b) bisa hujjar kin yin wani abu akai daga ofishin sauraron koken cikkn lokacin da aka dibar musu na daukar mataki.

(c) Saka lokacin zama domin sauraron koken kwastoma da jami'i kamfani wuta.

(d) Idan mai korafi bai samu Halartar zama a ranar da aka tsayar domin yin hakan ba,to tawagar na iya yin fatali da karaf,ko kuma idan akwai kwakkwarar hujja ta rashin bayyanr tasa to ana iya sake saka wani lokacin zaman koma a gudanar da zaman ta yanar gizo.

(2) Dole ne bawa kowanne korafi lokacin sauraron yadda ya dace sannan kuma a dauki mataki a tsakanin watanni biyu daga lokacin shigar da kara.

(3) Ana iya dage lokacin cigaba da zaman sauraron korafi idan har akwai kwakkwarar bukatar yin hakan.

(4) A inda aka samu akasin rashin yanke hukunci akan lokacin da aka kayyade a sama,to za'a iya yiwa kwastoma bayani a rubuce.

(5) Idan aka samu wani korafi Mai bukatar nutsuwa da yanke hukunci hakan ba'a so dai ya wuce wa'adin watanni biyu da aka gindaya a baya

(6) Duk wani zana Shugaban tawagar zai jagorance shi tare da karban duk wani bayani daga wajan sakatare,idan an samu wani mamba bai halarci zaman ba za'a cigaba da zama batare da dakatawa ba.

51. (1) Da zarar an kammala zaman,idan har tawagar ta gamsu da dukkanin wani koke da aka shigar zata rubuta hakan ga kamfani rarraba lantarki da kuma kwastoma,yayin yanke hukunci zata iya...

(a) Mayarwa da mai korafi duk wani kudi da aka caja ba bisa kaida ba.

(b) Gyara a inda aka samu akasi cikin korafi.

(c) Shawo kan matsalar tun daga tushe.

(d) Janye duk wani and aiki mai hatsari da aka gabatar.

2 idan kuma tawagar taga korafin bashi da tushe zata iya watsi dashi da kuma sanar da hakan a rubuce ga kamfani da kuma mai karar.

(3) duk wani hukunci na tawagar zai zama bisa Kada kuria ne daga mambobin ta,a inda aka samu kunnan doki kuwa sai Shugaba ya ya ke hukunci.

(4) Dole duk wani hukunci ya zamo a rubuce kuma dauke da sa hannun mambobin da suka halarci zaman.

(5) Za'a gabatar da lokacin zama, hukunci da duk wani abunda ya kamata ga Mai korafi da kuma kamfani.

(6) Dole ne kamfani ita kuma tayi aiki da hukuncin da tawagar ta zartar a tsakanin lokacin da aka ware,da kuma sanar da tawagar yin aiki da hukuncin ko akasin hakan idan an samu tsaiko cikin kwanaki biyar na aiki.

52. (1) Duk wanda bai gamsu da hukuncin ba zai iya sake daukaka kara cikin kwanaki 10 na aiki daga lokacin da aka gabatar da hukuncin a bisa irin su tsarin da hukumar ta tanadar.

(2) Hukumar zata iya sauraron karar da aka daukaka koda ya nuna wuce lokacin da aka ware na daukakawar idan har ta gamsu da hujjar data dakatar da yin hakan a farko.

(3) Hukumar bazata yi duba akan korafin kwastoman da aka yanke hukunci ya biya kamfani wasu kudi ba har sai in ya biya din.

(4) A inda aka samu akasin rashin daukaka kara, za'a dauki matakin da zai janyo wasu tara har sai an kammala

(a) Hadawa,datsewa, dubu 10 a kowacce rana.

(b) SabonMita,duba ta,gyara ta da bypass dubu 10

(c) Gyaran transformer, karfin wuta ,sauyawa dubu 10

(d) Kudin wuta,biya,gyara dubu 10

(e) Tara ta kwastoma,ko ihisani kamar yadda yazo bisa tsarin kaidoji zai janyo dubu 10

(f) batutuwan tsaro dubu 10

53. tawagar  zata gabatar da jadawalin koken da ta karba na rubu'i ga hukumar.

## SASHI NA BIYAR

### Tsarin Aikin Kula da Kwastoma

54. (1) Idan aka samu korafi daga kwastoma cikin Awanni aiki cewa lantarkin gidan sa ta dauke, jami'an kamfani zasu kai ziyara gidan cikin Awanni 24 da mika korafin domin gano matsalar,idan har aka samu matsalar tazo daga bangaren samun matsalar kayan aiki na kamfani,to za'a yi amfani da wannan tsari.....

(a) Samun matsala daga Fuse din kamfani -Za'a canja fuse din,sannan a gyara wutar cikin Awanni 24 da mika korafin.

(b) Karamar matsala daga kayan aikin kamfani -Za'a gyara matsalar da kuma gyara wutar cikin Awanni 24.

(c) Wata matsala ta daban daga kamfani - itama za'a shawo kan matsalar da kuna kuma gyara wutar cikin Awanni 48 da daukewar ta.

(2) Kamfanin rarraba lantarki zai janye daga yin wani yunkuri aiki da aka bayyana a sama idan har daya daga cikin wananna ya faru.

(a) Kwastoma ya gaza sanar da kamfani game da matsala.

(b) Daukewar wutar ta faru ne sakamakon yanayin wayar wutar kwastoma.

(c) Saboda yanayin matsalar,bazai yiwu kamfani ta iya magance ta ba cikin Awannin da aka bukata.

55. (1) Idan aka samu kwastoma ya bukaci karin sabon hada wuta a cikin muhallin sa, kamfani zata yi hubbasa wajan yin hakan ta hanyar sa masa sabuwar mita cikin kwanaki 10 na aiki da mika bukatar idan dai har...

(a) kamfani taje ta duba wajan da tabbatar da yiwuwar yin hakan

(b) Ta kuma amince da sake hadawa kwastoma din wutar.

56. A inda kwastoma kuma ya bukaci kamfani data samar da wasu kayayyaki aiki na musamman domin hada mishi wuta, kamfani nada damar rubuta jerin jadawalin kayan cikin kwankin aiki biyar .

57. A inda kuma kamfani zata katse wuta domin yin wani aiki,ana bukatar ta sanar da kwastoma kafin takai ga katse wutar akalla kwanaki uku na aiki

58. Idan aka samu korafi daga kwastoma na irin wutar da aka kawo mai karfi fiye yadda yake a tsarin kamfani kamar in wutar (tayi yawa,ko kadan ko ta kona kayan aiki) jami'in kamfani zai ziyarci muhallin kwastoma cikin Awanni 24 ,idan kuma har ba'a iya maganace matsalar ba a yayin ziyarar to a tabbatar da an dauki duk wasu matakan tsaro da kariya  akan korafin.

59. Idan aka samu korafi daga kwastoma ga kamfani akan aikin da mita take bisa kuskure, jami'in kamfani zai ziyarci muhallin kwastoma cikin kwanaki uku da shigar da korafi daga nan saiya gwada mitar da kuma yin gyaran da ake bukata  idan kuma kamfani taga ya kamata a sake wani sabon aiki ne dai duka yana dakyau tayiwa kwastoma bayani.

60. kwastoman da aka yanke wa wuta sakamakon rashin biyan kudin kudin wutar lantarki ko wasu kudade da suka shafi harkar wutar, za'a mayarwa kwastoma wutar shi,cikin Awanni 24 da kammala biyan.

61. Yayin da kwastoma ya bukaci sake daidaita masa zaman mitar sa,ya kuma biya kudin aikin hakan ga kamfani, za'a yi aikin ne cikkn kwanaki biyar na aiki ga muhallin kwastoma.

62. Idan kwastoma ya mika korafi ga kamfani cewa mitar da aka gyara bata aiki yadda ya kamata,kuma ya mika korafin a Awanni aiki,to kamfani zata ....

(a) ziyarci muhallin kwastoma cikin Awanni 24 domin duba mitar.

(b) Idan zai yiwu za'a gyara matsalar,sai dai idan kuma laifin daga waja. kwastoma yake.

63. Kamafani zata janye daga kin yin  aikin idan dai har aka samu wadan nan dalilai.....

(a) Idan aka samu cewa mitar tana aiki daidai.

(b) Idan aka hana kwastoma damar duba mitar.

3. A inda aka samu matsala daga mita , kamfani zata yi hubbasa wajan samar da wata mitar ko gyara akai cikin kwanaki biyu da mika korafin da Kwastoma yayi.

4. idan kuma aka samu mitar tana aiki ne bisa tsari na bashi,to kamfani zata sanar da kwastoma sannan kuma ta gabatar da gyaran da ake bukata.

5. Idan kuma aka samu mita na aiki ne a tsarin bashi kuma kwastoma bai san da hakan ba,to kamfani bazata caje shi komai ba,sannan zatayi gyara akan hakan.

6. Idan aka samu inda aka sakawa kwastoma mita bisa tsarin farawa da bashi za'a fadawa kwastoma hakan kafin a warware hakan a gaba.

63. Dole kamfanonin rarraba lantarki su dinga bibiyar aikin mitar yankin da suke akalla kowanne wata ko sau daya cikin wata uku sann kuma zasu duba idan an samu masu satar wuta.

64. Wadan nan dalilai zasu iya sawa kamfani ta dakata daga gabatar da aikin da aka bukaci tayi da farko....

(a) idan kwastoma yace baya son aikin daya bukata da farko daga kamfanin.

(b) Ba'a bawa kamfani irin bayanan data bukata ba.

(c) Kwastoma yaki biyan wasu kudi ga kwastoma kamfani wanda kuma suna cikin abinda zasu kai ga yin aikin.

(d) hujjar da kamfani zataki gudanar da aikin da aka bukace ta akan lokaci saboda ..

(i) Sauyin yanayi

(ii) Yajin aiki ga maaikatan kamfani.

(iii) Rashin bada dama ga jami'an kamfani wajan zuwaa ga inda ake bukatar aiwatar da aikin akan mitar.

(iv) Matsala akan bangaren fasahar da baza'a iya maganace taba nan take.

65. (1) Kamfani zata ringa duba akan irin ayyukan ta ga kwastoma kamar yadda yazo cikin kaidojin ta.

(2) Kamfani zata ringa turawa hukumar rahoton tsarin tafiyar da Kwastomomin ta .

(3) Za'a dinga tura tsarin mika rahoton ga hukumar kamar yadda yazo a kaida ta 6 na wannan kaidoji cikin kwanakin aiki 10.

(4) Hukumar zata ringa wallafa hubbasar aikin kowanne kamfani da tsarin tafiyar da Kwastomomin su.

66. Dukkanin kamfanonin rarraba lantarki zasu....

(a) Sanar da Kwastomomin ta wanzuwar bangaren sauraron koke da kuma irin ayyukan su.

(b) Haka kuma zasu wallafa tsarin aikin kula da kwastomomin su a kafar su ta yanar gizo dama ajiye takardun kofin ga kwastomomi.

## JADAWALI NA DAYA

### 1) Hada wuta ta sama: mai fuska daya

| S/N | KAYAN AIKI | NA'URA | ADADI |
|---|---|---|---|
| 1. | Wayar alminiyom PVN 16 $mm^2$ | Mita | Jumi'i zai bayyana abunda ake bukata idan ya kamala bincike |
| 2. | 30 ampere miniature circuit (MCB) – TP | No | 1 |
| 3. | Pin insulator | No | 1 |
| 4. | Katako | No | 1 |
| 5. | 60 ampere cutout fuse | No | 1 |

### 2) Hada wuta ta sama" fuska uku

| S/N | KAYAN AIKI | NA'URA | ADADI |
|---|---|---|---|
| 1. | Wayar alminiyom 16 $mm^2$ PVN | Mita | Jumi'i zai bayyana abunda ake bukata idan ya kamala bincike |
| 2. | 60 ampere miniature circuit breaker (MCB) – TP da pin insulator | No | 1 |
| 3. | Pin insulator | No | 2 |
| 4. | Katako | No | 1 |
| 5. | 60 ampere cutout fuse | No | 3 |

### 3) Hada wuta ta kasa mai fuska daya

| S/N | KAYAN AIKI | NA'URA | ADADI |
|---|---|---|---|
| 1. | 2 x 16$mm^2$ kebil na cooper armoured-(SWA) | Mita | Jumi'i zai bayyana abunda ake bukata idan ya kamala bincike |
| 2. | 16$mm^2$ cable socket | No | 8 |
| 3. | 60 ampere cutout fuse | No | 1 |
| 4. | 30 ampere miniature circuit breaker (MCB) | No | 1 |
| 5. | Katako | No | 1 |
| | Bimetallic line tap | No | 2 |

### 4) Hada wuta ta kas fuska uku

| S/N | KAYAN AIKI | NA'URA | ADADI |
|---|---|---|---|
| 1. | 4 x 25$mm^2$ cooper armoured cable (SWA) | Mita | Jumi'i zai bayyana abunda ake bukata idan ya kamala bincike |
| 2. | 25$mm^2$ cable socket | No | 8 |
| 3. | 60 ampere cutout fuse | No | 1 |
| 4. | 30 ampere miniature circuit breaker (MCB) | No | 1 |
| 5. | Katako | No | 1 |

| | | | |
|---|---|---|---|
| | Bimetallic line tap | No | 4 |

5) **Karin adadin kayan aiki (1 span na mita 45)**

| S/N | KAYAN AIKI | NA'URA | ADADI |
|---|---|---|---|
| 1. | 8.6 na kakkarfun pol din kankare | No | 1 |
| 2. | 150mm2 alminiyum alloy conducto | Mita | - |
| 3. | Stay rod | No | 1 |
| 4. | Stay wire | Mita | 10m |
| 5. | Stay block | No | 1 |
| 6. | Stay insulator | No | 1 |
| 7. | Shackle insulator | No | 8 |
| 8. | d-iron | No | 4 |
| 9. | Stud | No | 4 |
| 10. | 5/8 by 9 bolt/nut | No | 8 |
| 11. | Washer | No | 16 |
| 12. | Extunsium strap | Pairs | 4 |

6) **High extension – 11kv link up (1 span na mita)**

| S/N | KAYAN AIKI | NA'URA | ADADI |
|---|---|---|---|
| 1. | 10.6m na pol din kankare | No | 2 |
| 2. | Kafa 6 na iron din channel | No | 2 |
| 3. | 150mm2 alminiyum conductor | Mita | 165m |
| 4. | Disk insulator | No | 6 |
| 5. | 6 bolt stain clamp | No | 6 |
| 6. | Adaptor clevis ball | No | 6 |
| 7. | Adaptor clevis socket | No | 6 |
| 8. | J-Hook | No | 6 |
| 9. | Stay wire | Mita | 30 |
| 10. | Stay block | No | 2 |
| 11. | Stay rod | No | 2 |
| 12. | 11kv Stay insulator | No | 2 |
| 13. | 5/8 x 12 bolt/Nut | No | 4 |
| 14. | 5/8 x 9 bolt/Nut | No | 4 |
| 15. | 5/8 x 4 bolt/Nut | No | 4 |
| 16. | 5/8 x 2 bolt/Nut | No | 6 |
| 17. | 35mm2 11kv single core XLPE cable | Mita | 45m |
| 18. | Terminating kids | Set | 2 set |

7) **High tension 33kv link up (1 span na 50 mita)**

| S/N | KAYAN AIKI | NA'URA | ADADI |
|---|---|---|---|
| 1. | 10.6m na pol din kankare | No | 2 |
| 2. | Kafa 9 na iron din channel | No | 2 |
| 3. | 33kv quanged isolator switch | Set | 1 |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 4. | Disk insulator | No | 18 |
| 5. | 6 bolt stain clamp | No | 6 |
| 6. | Adaptor socket tongue | No | 6 |
| 7. | Adaptor socket clevis | No | 6 |
| 8. | J-Hook | No | 8 |
| 9. | Terminating strap | No | 6 |
| 10. | 5/8 x 12 bolt/Nut | No | 6 |
| 11. | 5/8 x 11 bolt /Nut | No | 4 |
| 12. | 5/8 x 9 bolt /Nut | No | 4 |
| 13. | 5/8 x 4 bolt/Nut | No | 4 |
| 14. | 5/8 x 2 bolt/Nut | No | 6 |
| 15. | 70mm2 bare cooper wire | Mita | 15m |
| 16. | 150mm2 alminiyom conductor | Mita | 160m |
| 17. | Stay wire | Mita | 30m |
| 18. | Stay rod | No | 2 |
| | 33kv Stay insulator | No | 2 |
| | Stay block | No | 2 |
| | 150mm2 33kv single core XLPE cable | Mita | 90m |
| | Terminating kits | Set | 2 |
| | 33kv tie straps | Pair | 2 |

## JADAWALI NA BIYU

### Bayani akan takardar kudin wuta

1. Sunan kwastoma

2. Lambar Asusun bankin kwastoma.

3. Adireshin kwastoma inda za'a dinga tura takardar.

4. Adireshin inda za'a dinga kai takardar kudin wutar ,idan ba daya bane da adireshin kwastoma.

5. Lambar mita da aikinta zai zama yana jikin adireshin kwastoma,idan kuma mitar ba guda daya bace za'a rubuta adireshin kowanne a jikin takardar.

6. Kwanan watan da aka rubuta takardar.

7. Adadin kwanakin da aka sha wutar.

8. Idan aka samu karin adadin yawan amfani da mita,shima za'a rubuta a jikin takardar.

9. Yanayi da adadin da mita ke sha.

10. Adadin da mita tasha a baya da na yanzu.

11. Kwanan watan aikin mita na baya da yanzu.

12. Alama dake tabbatar da ko lissafin mita na yanzu da wanda ya gabata daidai ne ko akasin sa.

13. Adadin yawan kudin da akasha akan mita.

14. Darajar adadin kudin da akasha akan takardar.

15. bayani da adadin duk abunda akasha na wuta.

16. Adadin biya na gaba ko bashin dake kan takardar baya za'a saka a gaba.

17. Adadin bashin yanzu dake kan mitar.

18. Wa'adin ranar kammala biya.

19. lambar waya na takardar da kuma na tuntubar yadda za'a iya biyan kudin.

20. Bayanin bangaren kula da korafe na kamfanin rarraba lantarki.

21. Takaitaccen bayanin yanayin biya,wannan ya hada da bayanin yadda za'a yi biya.

22. Bangaren dake da alhakin kula da kwastoma.

23. Kudin dake kan kwastoma (A-E)

24. Kamafani zata iya kara wasu bayanai jikin takardar ta ko kafar yanar gizon ta,amma ta tabbatar da bata cire komai daga bayanan abunda ya gabata ba.

## JADAWALI NA UKU

## Tsarin aikin karban korafin kwastoma



**JADAWALI NA HUDU**

Takarda ta 1 jadawali na 1

Rigista kan matsala/korafi

Lamabr Korafi:_____________________ (Ofishi zai bayar)

Lamabr Korafi:_____________________ (Ofishi zai bayar)

Lambar rigistar mai korafi a CCU (DISCO) CCU/Code No:

Kwanan Wata:____________________________________

1. Suna da adireshin mai korafi ______________________________________________
2. Lambabobi wayar mai korafi_______________________________________________

| **Wacce irin matsala ce** | **Kutse (1)** | **Karfin wuta (2)** | **Yawa akan layi (3)** | **Mita (4)** | **Kudin wuta (5)** | **Katse wuta (6)** | **Jinkiri wajan hada sabon wuta (7)** | **Sauran bayani mai muhimmanci (8)** |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |

4. takaitaccen bayani akan matsala

5. duk wani bayani mai muhammci

6 kwanan watan shigar da korafi sa hannun mai korafi ____________

_____________________________ za'a yage nan __________________________________
wanan bungaren takadar kwastoma ne zai rike

Lambar korafi da kwanan wata (Ofishi zai bayar)

Lambar kwastoma (Ofishi zai bayar)

1. Sunan kwastoma ______________________________________________
2. Takaitaccen bayani akan korafi ___________________________________
3. Kwanan watan da ake son warware matsalar__________ ofishi zai bayar

Saka hannun jami'in daya karbi korafin

(Kar a manta a suka lambar korafi a duk wani batu na gaba)

**JADAWALI NA BIYAR**

**Tukarda ta 2**

Rahoton mai korafi

______________________________________

Wata da shekarar

| Sunan kamfanin rurruba lantarki | Sun an rass ans a | Adadi korafi wuta a tsare | Adadin tawan korafin da aka karba a wata | Lokaci da addadin kwanakin da aka warware matsalar (mofikaranci, mafitawa da tsaka-tsaki | Adadin korafin dake teburin C da aka warware | Adadin korafin dake teburin D daba'a warware ba | Adadin korafe korofen suke layi wanda ba;a warware ba har zuwa karshen wata | | | | | | | Dalilin rashin warwaresu |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | | | Fiye da wata 6 | Wata 3-6 | Wata 1-3 | Wa ta 1 | Wata adadi | | | |
| A | B | C | D | E | F | G | H | I | J | K | L | M | N | |
| | | | | | | | 1<br>2<br>3<br>4<br>5<br>6<br>7<br>8 | | | | | | | |

Wannan takarda kanfani da tawaga duk zasu iya amfani da ita

Jadawalin korafi:

1) Kutse
2) Jarfin wwuta
3) Yawa akan layi
4) Mita
5) Kudin wuta
6) Katse wuta
7) Jikiri wajan hada sabon wuta
8) Sauran korafe-korafe

**JADAWALI NA SHIDDA**

**Takardar sa ido ta wata**

Yanayin saiso akan aiki na wata

| Bayani | wa'adi | Adadi cikin wata | Adadin koken da aka iya warwarewa | | % na adadi | Adadin da ba'a iya cimma ba kan wa'adi | % na adadi |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | Adadin korafin dab a a magnce ba | Wanda discos ta magance | | | |
| 1. Idan ba'a hada wuta a muhallin kwastoma ba | Daukar mataki cikin a wanni 24 | | | | | | |
| a. Daina akain fuse din kwastoma | Samar da wuta cikin awanini 24 | | | | | | |
| b. koramar matsala | Magance ta cikin awanini 24 | | | | | | |
| c. Sauran matsaloli | Magance su cikin cikin awanini 48 | | | | | | |
| 2. Samar da wuta akan mita | Cikin kwanaki 10 da aika mika bukata | | | | | | |
| 3. Kayyade adadin karba yayin hada wuta | Yin hakan cikin kwana 3 ko biyar | | | | | | |
| 4. Sanar da samun akasi a aikin da aka shirya yi | Bada sanarwa cikin kwanaki 3 | | | | | | |
| 5. Korafi akan | Ziyara cikin | | | | | | |

| | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| karfin wuta | awanin 24 da daukar mataki 5 | | | | | | |
| 6. Matsala akan mita | Ziyara cikin kwanaki 3 da korafi | | | | | | |
| 7. Sako mayar da wuta bayan an yanke saboda rashin biya | Mayarwa cikin awanin24 | | | | | | |
| 8. Sake daidaita mita | Ziyara cikin 5days don dubawajan aiki | | | | | | |
| 9. Muttani kun mutsalar da ake samu a mitar da aka biya | Ziyara ikin kwanaki biyar dayin korafi | | | | | | |
| 10. Duba akan tsarin aikin mita | Akalla kowane wata uku | | | | | | |

An haltama da cimma wannan ka'idoji na hukumar rarraba lantarki bias umarnin hukumar a ranar 29 ga marsi 2023

______________________

**Sunusi Gara**
**Chairman**